# Surah 86: Altariq - سورة الطارق

بسم الله الرحمن الرحيم

[86:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

وَالسَّمَاءِ وَالطَّارِقِ ١

[86:1] Ina rantsuwa da sama da Al-tariq.

وَمَا أَدْرَاكَ مَا الطَّارِقُ ٢

[86:2] To, ko ka san abin da ake nufi da Al-tariq?

النَّجْمُ الثَّاقِبُ ٣

[86:3] Shi ne tauraron nan mai tsananin haske.

إِن كُلُّ نَفْسٍ لَّمَّا عَلَيْهَا حَافِظٌ ٤

[86:4] Lalle ne, babu wanda ba a yi masa tsaro ba sosai.

فَلْيَنظُرِ الْإِنسَانُ مِمَّ خُلِقَ ٥

[86:5] To, mutum ya duba yadda aka halitta shi.

خُلِقَ مِن مَّاءٍ دَافِقٍ ٦

[86:6] An halitta shi ne daga wani ruwan da aka fitad da shi.

يَخْرُجُ مِن بَيْنِ الصُّلْبِ وَالتَّرَائِبِ ٧

[86:7] Daga tsakanin qashin baya da haqarqari.

إِنَّهُ عَلَىٰ رَجْعِهِ لَقَادِرٌ ٨

[86:8] Lalle ne Shi mai ikon iya tayar da shi ne.

يَوْمَ تُبْلَى ٱلسَّرَآئِرُ ٩

[86:9] Ranar da za bayyanar da dukan asirai.

فَمَا لَهُۥ مِن قُوَّةٍ وَلَا نَاصِرٍ ١٠

[86:10] Ba zai sami wani iko ba, ko wani mai taimako.

وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلرَّجْعِ ١١

[86:11] Ina rantsuwa da sama ma'abuciyar ruwan.

وَٱلْأَرْضِ ذَاتِ ٱلصَّدْعِ ١٢

[86:12] Da qasa ma'abuciyar tsaga (*domin tsiro*).

إِنَّهُۥ لَقَوْلٌ فَصْلٌ ١٣

[86:13] Wannan muhimmin magana ce daki-daki.

وَمَا هُوَ بِٱلْهَزْلِ ١٤

[86:14] Wanda ba za a yi wasa da shi ba.

إِنَّهُمْ يَكِيدُونَ كَيْدًا ١٥

[86:15] Suna qulle-qullen kaidi.

وَأَكِيدُ كَيْدًا ١٦

[86:16] Kuma Ni ma Ina mai mayar da martanin kaidi.

فَمَهِّلِ ٱلْكَٰفِرِينَ أَمْهِلْهُمْ رُوَيْدًۢا ١٧

[86:17] Saboda haka, ka dai jinkirta wa kafirai, na wani dan lokaci.